## SŨRATUL KÃRI'A سُورَةُ القَارِعَةِ

Tana bayãnin Rãnar Kiyãma wajen hãlin fitar mutãne daga kaburbura da hãlãyen ƙasa da rabuwar mutãne bãyan hisãbi, wasu zuwa Aljanna wasu zuwa wuta, a bãyan bũsar ƙaho ta biyu.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Mai ƙwanƙwasar (zukata da tsõro)!

*2.* Mẽ ne mai ƙawanƙwasa?

*3.* Kuma me ya sanar da kai abin da ake ce wa mai ƙwanƙwasa?

*4.* Rãnar da mutãne za su kasance kamar 'ya'yan fãri mãsu wãtsuwa.

*5.* Kuma duwãtsu su kasance kamar gãshin sũfin da aka sãɓe.

*6.* To, amma wanda ma'aunansa suka yi nauyi,

*7.* To, shi yana a cikin wata rayuwa yardadda.

*8.* Kuma amma wanda ma'aunansa suka yi sauƙi (bãbu nauyi),

*9.* To, uwarsa Hãwiya ce.

*10.* Kuma me ya sanar da kai me ne ita?

*11.* Wata wuta ce mai zafi.

ٱلْقَارِعَةُ ١

مَا ٱلْقَارِعَةُ ٢

وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا ٱلْقَارِعَةُ ٣

يَوْمَ يَكُونُ ٱلنَّاسُ كَٱلْفَرَاشِ ٱلْمَبْثُوثِ ٤

وَتَكُونُ ٱلْجِبَالُ كَٱلْعِهْنِ ٱلْمَنفُوشِ ٥

فَأَمَّا مَن ثَقُلَتْ مَوَٰزِينُهُۥ ٦

فَهُوَ فِى عِيشَةٍ رَّاضِيَةٍ ٧

وَأَمَّا مَنْ خَفَّتْ مَوَٰزِينُهُۥ ٨

فَأُمُّهُۥ هَاوِيَةٌ ٩

وَمَآ أَدْرَىٰكَ مَا هِيَهْ ١٠

نَارٌ حَامِيَةٌۢ ١١